* 💧DARK LUST💧*
_*(Hot love and destiny)*_

*Fauziyya Tasiu Umar*

_Bismillahir Rahmanur Rahim_

*Page 1-2*

*Mafari*

Ƙauyen Wanzamai dake cikin wani local government a cikin garin Kano a Kano ta Kudu, jama'ar dake rayuwa a wannan gari ba za su haura dubu ɗaya ba, Allah ya azurta su da ƙasar noma da kuma arziƙin duwatsu da ke ɗaukar hankalin 'yan birni, da sukan ɗauko ƙafa su taho kawai domin ɗaukar hotuna da short video da za su samu na trending a duniya.
Yau ta kama ranar Lahadi ce kasancewar tazo daidai da ƙarshen hutun zangon karatu da akayi ɗalibai sai shirye-shiryen komawa makarantu akeyi, cikin wani babban gida me ƙofa ƙofa zubin ginin gargajiya, ƙofar Mal Alasan wata yarinya ce da shekarunta bazasu wucce 14 ba tsugunne gaban murhun duwatsu tana iza wutar karar da take ci da dukkan alamu wani abu ake so ya dahu a cikin tukunyar.
Faheemah! Faheemah!! Ke Faheemah ina kika shiga ne kizo ki ƙarasa haɗa kayan nan naki nasan duk inda Mal yake yanzu hankalinsa na kanki yamma ta fara daganan zuwa makarantarku da nisa kuma" Miƙewa yarinyar da dukkan alamu itace take amsa wannan suna na Faheemah tayi ta nufi ɗakin da Muryar take tasowa ta duƙa ta shiga domin itan doguwa ce akan ƙofar wata matashiyar mata ce da itama shekarun nata bazasu haura daga 30 ba zaune ta mimmiƙe ƙafa da uban ƙaton ciki a gaba da alama dai gaf take da haihuwa.

Zama tayi a gaban adakar dake gaban wannan mata tace "Inna sannu ya jikin? Nifa dama nace Miki kibar haɗa kayan nan Inna Nifa kawai naji kamar kada na tafi na barki a wannan halin kina ganin irin zaman da kukeyi da Babarsu Lamimi sannan duk matan gidannan ba sanmu sukeyi ba kowa ita yake goyon baya duk rashin kirkin da zatayi Miki kece mars gaskiya, nidai bari Mal ya dawo na faɗa masa ya barni na zauna dake bayan kin haihu na tafi"
Kamo hannunta Inna Dije tayi tace "Banda abinki Fahim Inna zaman naki zai hana Allah ikonsa ne? Kinga burina a duniya kiyi karatun boko me zurfi ki zama likita kodon kula da matsalolin mata fahim Inna Nasha wahala a haihuwarki malaman asibiti sun wulaƙantani nida Babanku da duk wani daya shafeni kawai don sunga daga ƙauye muke sukaƙi karɓarmu har Saida kanki ya fara fitowa sannan wata likita ta shigo inda nake taga halin da nake ciki ta ɗaukeni ta shiga dani ɗakin haihuwa tanata masifa ta zage ta taimaka min Allah yasa dani dake munada rabon shan

iskar duniya kikazota gashinan tun lokacin har yanzu bamu huta ba" kullum idan mahaifiyarta na bata wannan labarin takanji tausayin kansu da kuma tsanar likitoci domin kuwa sun nunawa Innarta rashin imani Amma babu komai tasan wataran zata wankewa Inna zuciya idan itama tayi karatu ta zama likita.

Sallamar Mal ce ta katse musu hanzari Inna tace “Sannu da zuwa Mal dama yanzu nake cewa duk inda kake kana hanya" cire hularsa yayi yace “Wlh Hadizatuq inacan daƙyar na samu wanda yasai akuyar nan shima rabin kuɗin ya bani yace rabin sai ranar kasuwa to yanzu dai zuwa Zamuyi mu tafi indai Allah yasa na kuma samun wasu kuɗi kafin ran kasuwar sai na ƙara mata guzuri nakai mata, Ince dai kin shirya Heeman Mal" ƙasa tayi da kanta tace “Na shirya Mal saidai Ni banajin tafiyar nan banason na tafi nabar Inna a wannan halin da take ciki" daƙuwa yayi mata yace “Ƙundun ubaki nace! tashi muje" miƙewa tayi sumsum ya ɗauki kayan dake cikin buhu suka fito tana waiwayen mahaifiyarta itama Inna Dije kallon ɗiyar Tata takeyi cike da kewa har suka fita daga ɗakin suka fito tsakar gidan matan gida da sukayi da'ira da'ira da kuma yara sa'o'inta da waɗanda basu kaita ba duk suka bisu da kallo can sukaji an sheƙe da dariya uwar Lamimi da take ita ce uwar gidan Mal Alasan tace “Ahayye nanaye kaga yan bokoko a wuta an fito za'a tafi Koyon yahudanci to Allah raka taki gona abinki ya ƙare a kanki keda uwarki" cak Faheemah ta tsaya Zuciyarta na suya duk abinda zaayiwa rayuwarta takan iya jurewa amma banda taɓa darajar iyayenta Inna Dije da Mal Alasan mutane masu kawaici da haƙuri domin Allah ita tasan duk yakanarta da haƙurinta da yan makarantar su suke faɗa bata kama sawun uwayenta ba domin kuwa data kama da ciwon ma da takeji a zuciyarta bazataji ba.

Waiwayowa Mal Alasan yayi ya hangeta can nesa tana tsaye ya kwala mata kira tare da cilla mata daƙuwa, ta tako da sauri ya kama hannunta Yace “Heeman Mal ki koyi juriya haƙuri da kawaici ita rayuwar gabaɗaya nawa take, yau ake dakai gobe da waninka za'ayi yau ina Kakarku Ina Mal Idi mahaifinmu ina ƙannenki na ɗakinku Hassan da Hussaini duk babu su, Heemah ina ƙawarki Hajara da kuka taso da ita, to idan kikayi haƙuri kema watarana labari zaki zama sai a faɗi alkhairinki bayan bake sukuma Mala'iku su rubuta Miki akai Miki yabon da kika samu a duniya cikin kushewarki, nidai roƙona dake na yau da kullum ne Faheemah ki nutsu kiyi abinda ya kaiki banda biyewa mugayen ƙawaye banda wasa kuma banda kwaɗayi ki tsaya inda Allah ya ajiyeki duk inda kikakai da kasawa wani yafiki kinfi wani, mu mutanen karkara ne kuma talakawa shiyasa bazakiga komai namu irin na ƴan ajinku yan birni ba kiyi haƙuri watarana sai labari"
Suna tafe yana mata nisihohin shi masu shiga jiki da zama a cikin ƙwaƙwalwa har suka isa inda zasu hau mashin ya kaisu cikin garin Rano daganan suka hau motar Tudun Wada kasancewar anan makarantar tasu Faheemah take, suna tafe tana kwance jikin Mahaifinta duk da ba daɗin

rayuwar makarantar tasu takeji ba amma takanso kasancewa a makaranta fiye da gidansu saboda gidansu gidan masifa ne a cewarta matan aure sunfi Ashirin a gidan su kuwa ƴaƴa sunkai ɗari banda waɗanda aka aurar da waɗanda suka mutu, a ƙofarsu ma su bakwai ne ƴaƴan Lantai wadda suke kira Uwar Lamimi su Shida sai ita a ɗakin babarta Inna Dije ita kaɗai koda Inna Dije ta haihu yakai bakwai ɗiyoyinta suna mutuwa itadai batasan meye yake faruwa ba amma takanji tun tana ƙarama idan Innanta ta haihu ɗan ya koma a gidan ana yan tsegungumin tayi amanta ta lashe, har yanzu tana neman fassarar wannan kalma duba da yanda ake kyararta da tsangwamarsu a gidan nasu sai take ganin kamar abin yanada alaƙa da wannan kalmar duk da har yanzu batasan ma'anar kalmar ba.

*Contact me 09031307566*

*Oum Hairan*